# 4 Kwanuka



| Tsarki |
|---|
| Abin da ake nufi da kwano |
| Amfani da kwanon zinare da na Azurfa |
| Wajen ci da sha- |
| Ba wajen ci da sha ba- |
| Amfani da kwanon da aka liƙe shi da azurfa |

## Kwanuka

**Kwanuka**

Abubuwan da ake ajiye ruwa ko wani abu a cikinsu

An halatta a yi amfani da kowanne kwano ko ƙwarya wajen ci ko sha da sauransu, amma banda kwanon zinare da azurfa, ga yadda bayaninsu yake:

## Amfani Da Kwanon Zinare Da Azurfa

### Wajen Ci Da Sha

Haramun ne a yi amfani da su, saboda faɗinsa (ﷺ): «Kada ku sha da kwanon zinare da azurfa, kada ku ci a cikinsu, saboda ta su ce (kafirai) a duniya, a lahira kuma tamu ce» (Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi). Da faɗinsa (ﷺ) «Wanda yake shan wani abu a cikin kwanon azurfa to yana kwankwaɗar wutar Jahannama ne a cikinsa» (Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi).



Butar azurfa saboda yin alwala



Amfani da kwanon da aka liƙe da azurfa



Sha da kwanon Azurfa



Ci a ikin kwano Zinare

https://www.al-feqh.com/ha

## Amfani Da Dwanon Dinare D Azurfa Ba A Wajen Ci Ko Sha Ba

An halatta a yi amfani da su ba a wajen ci ko sha ba, kamar yin alwala da sauransu, saboda hadisin da ya gabata ya taƙaita hanin a kan ci da sha, kuma ya tabbata cewa Ummu Salama «Allah ya yarda ita tana da wani asusu na azurfa, a cikinsa akwai gashin kan Manzon Allah» (ﷺ). (Bukhari ne ya ruwaito shi)

## Amfani Da Kwanon Da Liƙe Shi Da Azurfa

Ya halatta a yi amfani da kwanon da aka liƙe shi da 'yar azurfa kaɗan don wata buƙata, saboda abin da ya tabbata cewa «akushin Manzon Allah (ﷺ) ya fashe, sai a ka sanya wata sarƙa ta azurfa a wurin da ya fashe ɗin». (Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi)

## Sanya kayan zinare ga maza

Ba ya hallata maza su sanya kayan zinare, saboda abin da ya tabbata daga Abu Musa Al-ash'ariy – Allah ya yarda da shi – ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce, «An haramta kayan alhariri da zinare ga mazan al'ummata, an halatta wa matansu» (Tirmizi ne ya rawaito shi).



https://www.al-feqh.com/ha